# SUNNAH NEWS NIGERIA

## Labaran Sunnah A Tafin Hannun ku

MUJALLAR SUNNAH DOMIN SANIN HALIN DA SUNNAH KE CIKI

DATE: Friday 22, December, 2017

## An Kammala Aikin Katafaren Dakin Karatu A Markazu Imamul Bukhariy Dake Kano

### Kungiyar Izala Tayi Gargadi kan Wasa Da Hakkokin Addini a Najeriya

**Kungiyar** tayi Allah wadai da Nuna tsangwama Ga Firdausi akan sanya Hijabi, Shugaban kungiyar **IZALA** Sheikh Abdullahi Bala Lau ya jawo hankalin hukumomi zuwaga wani labari da ya yadu akan wata daliba musulma, mai suna Amasa Firdaos, wacce ta kammala karatunta na zama lauya amma aka hanata samun shaida saboda ta saka hijabi.
Sheikh Bala Lau yayi gargadin cewa addini bai taba zama ginshiki ko mizani ba a tsarin gwamnatin Naijeriya. Saboda haka, muna jawo hankalin mahukuntan kasar, malamai da shuwagabanni da masu alhakin daukan ma'aikata ako wani sashi da sauran jaami'an kasar da su kiyaye sanya banbancin addini a matsayin mahangar duba cancantar 'yan kasar a kowane irin lamari musamman duba da yawan addinan dake kasar.

**An** kammala aikin dakin karatu (library) a **Markazul Imamul Bukhari** dake Rijiyar Zaki a Kano Nigeria karkashin jagorancin daya daga cikin manyan maluman Sunnah na wannan kasa Dr. Muhammad Sani Umar Musa Rijiyar Lemo.
Wannan dakin karatu yana dauke da manya-manyan litattafai na addini na fannonin ilmi daban-daban wanda aka kashe miliyoyin nairori.
Manazarta na hasashen cewa tabbas idan ma'abocin son karatu da bincike yayi sa'ar shiga wannan dakin karatu hakika ba zai so fitowa ba.
Hakika an tara littafai iri-iri a wannan dakin karatu. Ya rage masu bincike su amfana da shi.
Allah ya sakawa Dr. da alkhairi da duk wadanda suka taimaka wajen samar da wannan library.
Mai Rahoto: ***Muhd Habib Adam***



Shugaban yaci gaba da cewa a yayinda muke kushe wannan Al'amari da nuna rashin dacewar sa, a gefe guda kuma muna taya sauran 'yan Najeriya neman ayiwa wannar dalibar adalci kuma a gurfanar da duk masu hannu a cikin wannan cin zarafi. Muna kara jaddada kira ga hukumomi da 'yan kasar da suyi koyi da sauran kasashen duniya domin wayewarsu takai har ga kyale kowa yayi mu'amala gwargwadon yadda addininsa ya tanadar ba tare da tsageranci ba ga dokokin ubangiji"
Mai Rahoto: **Hassan Auwalu Ya'u**

***SUNNAH NEWS NIGERIA – LABARAN SUNNAH A TAFIN HANNUNKU***

**Sabuwar Tashar Sunnah News TV Tana Kan Hanya**

**A yanzu** dai tuni dandalin Sunnah News yayi nisa wajen samar muku da sabuwar tashar talabijin wadda zaku iya samu a wayoyin ku, ana saran fitowarta cikin mako mai zuwa.

**Darulfirk.com Takuce Domin Yada Sunnah Cibiya** guda daya tilo wadda take kawo muku karatuttukan maluman Sunnah daga wurare daban-daban a kowane lokaci, aciki da wajen kasarmu Nigeria.
http://facebook.com/darulfikrng

**SUNNAH NEWS NIGERIA DOMIN AMFANUWAR MUSULMAI**

Ku biyo mu ta: http://sunnahnewsnigeria.wordpress.com http://facebook.com/sunnahnigeria.ng http://twitter.com/sunnahnigeria 09035830253,08066989773, 08149332007, 08168015170

## Izala Ta Bude Sabon Masallacin Jumu'a A Jihar Zamfara



**A ranar Jum'ah** (15-12-2017 daidai da 26 Rabi'u Auwal 1439ah) ne Kungiyar Jama'atu Izalatil Bidi'ah Wa Iqamatis Sunnah ta jahar Zamfara ta buɗe sabon Masallacin Juma'ah a garin Bela na ƙaramar hukumar mulkin Bunguɗu.

Shi dai wannan masallaci, Marigayi Alh. Yaro Bela ne ya bada kyautar filin ga Ahlus Sunnah a lokacin da ake gabatar da sallah a ɗakinsa na aje mota wanda Sheikh Habibu Jibril yayi hanya wata mata ta gina masallacin domin neman lada ga Allah.

A wurin Sallar Juma'ar ta a Masallacin wadda Liman Abdullahi Salisu Aleiru ya jagoranta,



## An Gabatar da Wa'azin Hadin Gwiwa Tskanin Nigeria da Nijar

**A ranar** Asabar 16/12/2017 an gabatar da gagarumin wa'azin hadin gwaiwa tsakanin wasu jihohi wanda suke kan iyaka biyu da kasashen Nigeria da Nijar jihohin sun hada da: Jigawa, Katsina da kuma Damagaran da Magarya ana yin wannan wa'azi ne duk bayan wata daya a Nijar sannan sai ayi a Nigeria bayan wani wata guda dayan a wannan watan an gabatar da wannan wa'azi a garin Maigatari na jihar jigawa.

**Cigaban Labarin Duba Shafi na 3**

an gabatar da Nasihohi da jawabai na musamman domin samun nasarar tafiyar da Masallacin a bisa tsarin Al-kitabu-was-Sunnah. Liman Abdullahi Alairu ya gabatar da khuɗubar ne mai taken "Mahimmancin karatun Al-Kur'ani da kula da shi", Inda a cikin Khudubar Liman Aleiru yayi Allah wadai da ɗabi'ar nan ta jefa Kur'ani cikin ƙazanta tare da addu'ar Allah ya tona asirin masu aikata waɗannan migun ɗabi'un da waɗanda ke da hannu ciki.

Mai Rahoto:
Comrade Abdullahi Salisu Faru

# DAGA MASALLATAN JUMU'AR MU

**Shiri ne** dake kawo muku jigon sakonnin hudubobin jumu'a da aka gabatar a masallatan jumu'a daban-daban a ciki da wajen kasarnan, shiri ne da Ammar Isah Nuhu Batagarawa ke shugabanta tare da taimakawar Basheer Journalist Sharfadi,
Shiri ne da yake da dimbin masu sauraro sannan zaku dinga jin halin da duniyar musulunci ke ciki a kowane mako ta cikin shirin, zaku iya samun wannan shiri da ma wadanda suka gabata a kowane lokaci a www.darulfikr.com
Domin daukar nauyi ko tallata hajar ku ta cikin shirin, ko kuma aiko da taku hudubar sai a tuntubi: 08035830253, 08066989773, 08149332007, dagamasallatanmu@gmail.com
http://facebook.com/masallatanmu.ng http://twitter.com/dagamasallatai




## Sarkin Musulmi Zai Tallafawa Marayu 200

**Sarkin musulmi** Sultan na Sakkwato, Alhaji Muhd Sa'ad Abubakar, zai dauki nauyi marayu 200 da suka rasa iyayen su a sanadiyar ta'addanci na Boko Haram a yankunan Arewa maso Gabashin kasar nan.
Sultan ya bayar da wannan sanarwa ne a yayin taron kwanaki uku na cibiyar musulmai ta mata da aka gudanar a kwalejin Umaru Shinkafi dake Sakkwato.
Taron ya samu mahalarta daga jihohi 19 na Arewa da kuma makociyar kasa wato Jamhuriyyar Nijar.

***Mai Rahoto:***
***Basheer Journalist Sharfadi***

## Izala NHQ Jos Tayi Kira Ga Gwamnatin Tarayya

**Shugaban** Majalisar Malamai na Jibwis mai sakatariya a Jos shine yayi wannan jawabi Sheikh Muhd Sani Yahya Jingir ya tunawa gwamnatin Shugaba Buhari da alkwuran da ta yiwa talakawa a 2015 Malamin yace "Talakawa da kan su su ka rika kokarin ganin Buhari ya samu mulki".
Bisa alkawuran da aka yi musu na gyara al'amuran Ilmi, Noma da kuma gyaran hanyoyi, Sheikh Jingir ya bayyana hakan ne yayin da ya halarci wani taro da dalibin makarantar kiwon lafiya suka shiya a Jos.

***Rahoto: Hussain Auwalu Ya'u***

## A Nigeria An Hana Wata Musulma Zama Lauya Mai Iya Aki A Kotu

**An hana** wata 'yar Najeriya da ta kammala karatun lauya zama lauya - mai iya aiki a kotu - saboda hijabin da ta saka wanda ake ganin ya saba wa dokar tufafin makarantar horars da lauyoyin kasar.
Shugaban makarantar horas da lauyoyi Isa Hayatu Chiroma ya shaida wa BBC cewa an hana Amasa Firdaus shiga dakin taron yaye lauyoyi ne saboda bata sanya tufafin da ya dace ba.
Ta ki ta cire hijabinta, tana mai cewa dole ta saka hular lauyoyi kan dan-kwalinta.

Rahotanni sun ce Firdaus ta bayyana matakin a matsayin wani abin da ya keta hakkinta na bil Adama. Wata mata dai ta wallafa wani sako a shafin sa da zumunta na Instagram inda ta yi korafin cewa masu kula da lamuran dokar Najeria sun yi wa wata "'yar uwa" wariya tana mai amfani da maudu'in #justiceforFirdaus.



# Birnin Kudus Rigimace Tsakanin Musulmai da Yahudawa –Dr. Sani Umar Rijiyar Lemo

**Fitaccen** Malamin addinin Islama a jihar Kano Sheikh Dr. Sani Umar Rijiyar Lemo yayi bayani kan mallakar birnin Kudus. A cewar Malamin, asali Musulmi ne keda hakkin mallakar birnin Kudus, ya yi bayanin tarihin kafuwar birnin tun shekaru 3000 kafin haihuwar Annabi Isah (A.A).
"Asalin birnin Kudus wasu larabawan kauye ne da ake kira Kan'aniyyun suka kafa birnin, kuma mutanan suna magana da harshen larabci, (tsohon harshen larabci) An yi yaki da larabawa a kan wannan birni"
"Shekaru 2000 kafin haihuwar Annabi Isah, Annabi Ibrahim yayi hijira zuwa wannan yanki tare da matarsa Sarah a wannan yanki da ake kira Falasdinu. Wadda matar Annabi Ibrahim ta haifi Ishaq, wanda shi kuma ya haifi Yakub, wanda tsatsonsa ke tukewa zuwa ga Annabi Muhammadu Sallallahu Alaihi Wasallam"
"Annabi Ibrahim da dan Ismail shi ne ya gina Masallacin Kudus mai alfarma,



Wanda shi ne masallaci na uku mafi daraja a wajen Musulmi. Annabi Ibrahim ya zabi birnin Kudus ya zama cibiyar mulki a wancan lokacin".
Malamin yayi bayani mai tsawo daga alkurani da hadisi, inda ya kawo tarihin Annabawan Musulnci da suka zauna a wannan birni tun daga Annabi Ibrahim da sauran Annabawa da dama, dan haka Kasar Falasdinu, kasa ce mai daraja a wajen Musulmi.
An taba baiwa Yahudawa damar kafa kasarsu a shekarar 1917, inda Ministan harkokin wajen Burtaniya na lokacin ya basu damar kafa kasarsu, inda yanzu Trump ya sake maimaita wancan umarni shekaru 100 bayan wancan umarni da aka basu.

An kafa kasar Isra'ila ne a shekarar 1948, inda tun a wancan lokacin ne ta dinga fadada kan iyakokinta da kasashen da ke makwabtaka da ita musamman yankin gabar yamma da kogin Jordan da sauran sassa da suka hada da birnin Sina'a da sauran yankunan Sham.
Abinda Trump yayi sabawa abinda majalisar dinkin duniya ta yi yarjejeniya akansa. Don haka, abinda Trump yayi a yanzu ba zai taba canza tarihi ba, domin asali Yahudawa ba su da asali akan Kudus. A cewar Dakta Sani Riiyar Lemo.

Mai Rahoto: **Ammar Bn Isah Nuhu**

## Kungiyar Izala Tayi Gargadi kan Wasa Da Hakkokin Addini a Najeriya

**Kungiyar** tayi Allah wadai da Nuna tsangwama Ga Firdausi akan sanya Hijabi, Shugaban kungiyar **IZALA** Sheikh Abdullahi Bala Lau ya jawo hankalin hukumomi zuwaga wani labari da ya yadu akan wata daliba musulma, mai suna Amasa Firdaos, wacce ta kammala karatunta na zama lauya amma aka hanata samun shaida saboda ta saka hijabi.
Sheikh Bala Lau yayi gargadin cewa addini bai taba zama ginshiki ko mizani ba a tsarin gwamnatin Naijeriya.
Saboda haka, muna jawo hankalin mahukuntan kasar, malamai da shuwagabanni da masu alhakin daukan ma'aikata ako wani sashi da sauran jaami'an kasar da su kiyaye sanya banbancin addini a matsayin mahangar duba cancantar 'yan kasar a kowane irin lamari musamman duba da yawan addinan dake kasar.

**Cigaba:** Wa'azin ya samu halartan malamai daga cikin gida Nigeria irin su shugaban kwamitin Mal. Hassan Sabo Babura, Mal Ibrahim Bn Yahya, Mal Ibrahim Ciroma B/kudu da sauransu Alarammomi Ustaz Kabir Hussaini Daura, ustaz Jazuli Nasiru Ibrahim Maigatari usatz Jamil Yusuf Daura, ustaz Umar Zakariyya Gumel da sauransu sai daya bangaren malamai daga Janhoriyar Nijar irin su: Mal Mukhtar Zindar, Mal Muhammad Musa Zindar, Mal Mu'azu Muhammad Magarya da dai sauransu dai Alaramma Mustafa Bande Albindawy. Anyi fara karatu lafiya kuma cikin yaddar Allah an gama lafiya.
A karshe shugaban kwamitin malam Hassan Sabo Babura sun zauna an sake sa wani Wa'azin a garin Matamaye a janhoriyar nijar ranar 13/1/2018 Allah ya nuna mana ameen.
Mai Rahoto: **Hussain Bn Zakariyya Maigatari**

## Majalisar Agaji Ta Jihar Oyo Ta Gabatar Da Babban Taronta Na Jiha

**Majalisar** Agaji ta jihar Oyo ta gabatarda taron ta wanda ta saba gabatar wa a dukkanin karshen Wata.
Taron ya gudana ne a garin Oyo a daya daga cikin Makarantun unguwar mallakar kungiyar Izala.
A ci gaba da yiwa majalisar garan bawul, Shugaban rundunar na jiha ya sauyawa wasu daga cikin jami'an office tareda basu takardar fara aiki kamar yadda ya bayyana a cikin huto.
Shuwagabannin kungiyar na wannan garin Sun samu damar halartar wajen taron a inda shugaban Kungiyar ya samu rakiyar Limamin Unguwar da wasu daga cikin jagororin kungiyar a garin na Oyo.
Da yake jawabi a madadin tawagar, Sheikh Ibrahim Oyo ya nuna farin cikinsa ganin cewar majalisar Agaji tana ziyartar lungu da sako a fadin jihar tana kuma ganawa da yan Agajinta.
**Mai Rahoto:** ***Muhammad Habib Adam GadonKaya***

# DAGA KASASHEN WAJE

## Zamu Tabbatar Da An Fassara Alkur'ani Mai Girma A Dukkan Yarukan Duniya -Turkiyya

**Ma'aikatan** harkokin addinin Turkiyya ta bayyana fassarar Alkur'ani mai girma zuwa wasu rayuka da suka hada da Bulgarian, Uzbek, da kuma wasu harsunan Afirka-Chewa da Shonan.

Wannan dai nada cikin yunkurin ma'aikatar na ganin akwai Kur'ani a dukkanin harsunan dake duniya.

Ma'aikatar ta bayyana cewar zata ci gaba da binciken yarukan da ba'a fassara litifin mai tsarki ba ta sanya a fasara.

Tuni dai aka bada umurnin aik litafin mai tsarki da aka fassara zuwa ga yankunan masu magana da harsunan domin rabashi da kuma karantar dashi.

## An Rufe Wani Masallachi A Faransa

**Wata kotu** mai suna Marsilya ta rufe masallacin As Sunna har na tsawon watanni shida a bisa umarnin gwamnan yankin Pierre Dartout.

Kotun ta bayyana cewar ta rufe masallacin ne saboda masallacin mallakar masu tsatsaurarar ra'ayine. Lawyan masaallacin Philippe Perollier ya bayyana cewar yayi mamaki kwarai ganin yadda kotun ta bada umarnin rufe masallacin da laifin yin  zafafan huduba a 2013.

A kasar dai tun rannar 13 ga watan Nuwanba 2015 da aka saka dokan ta baci dalilan ta'addanci an dauki matakai da dama da suka hada da rufe masallatai. An dai bayyana cewar an rufe kusan masallatai 19 yayin da ba'a rufe coci ko daya ba a Kasar.

## Kotu Ta Soke Yin Saki Irin Na Addinin Musulunci a Turai

**Babbar kotun** Turai ta warware saki irin na Musulunci da wani dan asalin kasar Syria da ke zaune a Jamus ya yi wa matarsa, tana mai cewa shari'ar Musulunci ba ta da gurbi a Tarayyar Turai.

Kotun ta tarayyar Turai ta ce kasashen na Turai ba sa bukatar amincewa da saki irin na Musulunci wanda kotunan ba su san da shi ba.

Wasu Musulmi sun yarda cewa idan mutum ya ambaci saki uku sau daya aurensa da matarsa ya rabu kwata-kwata. Wannan shi ne karo na farko da aka taba yanke irin wannan hukunci a Turai.

## 'Yan Sanda Sun Kama Malaman Makarantar Islamiyya Biyu (2) Da Dalibai Guda Dari (100) a Kasar Kenya

**'Yan Sanda** a kasar Kenya sun kai samame wata makarantar addinin Islama da ke birnin Mombasa inda suka kama malamai biyu da kuma wasu yara 100 inda suka ce zasu kare lafiyar su.

Jami'an tsaron sun bayyana makarantar a matsayin wani sansanin da yara ke samun horon da ke mayar da su masu tsatsauran ra'ayin da ke mayar da su 'yan ta'adda.

Kakakin 'yan Sanda ya ce sun dade suna sanya ido a Makarantar kafin daukar mataki akai.

Sheikh Hassan Omar, jami'i a Majalisar limaman kasar ya ce cikin 'yan sandan da suka kai samamen harda 'yan kasashen waje.

# SANARWA DA KUMA SAKONNI

## Musulmar Farko Najat 'Yar-Takarar Kujerar Majalisar Dokoki

**Ta kasance** mace ta farko da ta samu kyaututuka har ta samu damar zuwa jami'a, kuma ta bada kyakyawar gudunmawa wajen ciyar da garin nasu gaba, Najat, tace "Ba ina son shiga majalisa bane don na zama mace ta farko musulma da ta zama 'yar-majalisa."

Sai dan inaso na kawo canji a cikin al'ummar mu, bana kuma fatar 'ya'yana suyi irin wahalar da iyaye na su kayi, koma a ce irin wadda nayi. Iyayen ta sun fito daga kasar Morocco, a lokacin da take 'yar shekaru 9 a shekarar 1990.

## Daura A Al-Majlisul Ilmi Dake Hotoro A Kano

**Kwamitin** daura na al-majlisul Ilmi na sanar da dalibai na ciki da wajen Kano cewa ta fara rijistar dalibai masu shiga daurar karo na 11 da ta saba gabatarwa a lokacin hutun makaranta za'a kammala rijistar a ranar laraba 08/04/1439, za'a fara gabatar wannan daurar ne kamar haka:

**Rana: Asabar 11/04/1439 zuwa 17/04/1439**

**Lokaci: 08:50 na safe zuwa karfe 01:00 na rana na dukkan ranakun**

**Wuri: Attarbiyya International College Tahfeez Hotoro**

**Kudin Rijista: ₦2,000**

Sanarwa: **Ammar Isah Nuhu**

## Samina Mai Taken Manufar Da'awa Da Yadda Ake Yinta A Garin Sokoto

**Lajnatud da'awa** dake Sokoto ta shirya Samina ta yini biyu mai taken manufar da'awa da yadda ake yinta wadda za'a gabatar kamar haka:

**Rana: Asabar da Lahadi 13&14, Jan, 2018.**

**Lokaci: 10:00 na safe zuwa 04:00 na yamma**

**Wuri: Babban dakin taro na makarantar Mus'ab bin Umair dake Sama Road Sokoto.**

**Ana yin rigistar shiga wannan daura a Sahaba Centre dake tsohuwar Kasuwa.**

**Kudin Rigista: ₦ 500**

Sanarwa:
**Nuraddeen Harande Mahe**

## Daura Akan Kirkirarrun Karya da aka Jinginawa Ibn Taimiyya A Garin Tsafe Dake Zamfara

**Kwamitin** masallacin Abu Huraira (R.A) dake Tsafe na sanar da al'ummar musulmi muhimmiyar daura da ya shirya gabatarwa mai taken **'kirkirarrun karya da aka jinginawa Ibn Taimiyya akan Mauludi'** wadda za'a gabatar kamar haka:

**Rana: Asabar, Lahadi, da Litinin 23 – 25, Dec, 2017**

**Lokaci: Magriba Zuwa Isha**

**Wuri: Masjid Abu Huraira dake Tsafe.**

**Za'a raba littattafan kyauta ga duk wanda ya samu halarta.**

Sanarwa: **Hashim Surajo Tsamiya**

**Sunnah News Nigeria Zata Gabatar Da Gagarumar Bita Domin Taya Murnar Auren Mal. Abubakar Abdussalam (Baban Gwale) kayi kokari kada ka sake a baka labari.**

**Bitar ta hada da Kwararru a shafukan sadarwa, Lauyoyi daga bangaren shari'a, Jami'an kiwon lafiya da kuma Maluman Addini, domin karin bayani sai a kira: 09035830253, 08149332007, 08149342004**